Cikin ikon Allah Yana Kara muza key din ya Bata wuta sai ta tashi Aiko suka zunduma ihu suna kokarin fita ta taga da hanzari ya rufe tagogin takaici ya ishi suhail suna yin gaba saiga tawagar sarki ta fito basuga komai ba sai sawunsu wani ihu sarki ya saki Yana gurnani kamar Zaki da hanzari suka koma hanyar dasuka fito dan bama yaso wani yaga titin sosai bare yai Sha'awar sa ransa a matukar bace suka juya gida gudu suke ekamar zasu tashi sama Ana iface iface da alkawarin ganin bayan su gaba daya idan ya kamasu huci kawai yake Wai harda dansa na cikinsa a wannan abun Ina baze yiwuba tabbas matarsa ta cuce shi Dan wannan abun dasa hannunta
```

Bari mu waiwayi su ja'e lokacin daya juya lafiya kalau ya karasa gidansa ya tattara matansa duka a wannan Daren dama bashi da yawan Yaya su ashirin da hudu ne matan nasa Yara Tara yayi musu bayanin musulunci sosai sun ji Dadi sun yarda sun gamsu da wannan addini yai musu bayanin yadda ze rabu dasu dukansu baze bar ko daya ba dukansu sunyi murna Banda tawargaji ita kadai ce Bata yadda ba Tai bakin ciki kamar me akanme ze rabasu da addininsu tun na iyaye da kakanni Nan ya Basu kalmar shahada suka karba gaba dayansu beyi nisa shima a addinin ba Dan Haka abunda ya sawwaka ya koya musu Amma yace su boye karsu bayyana sai angama komai

Ya shiga dakinsa ya kwanta abunsa Yana shiga ta wargaji ta fice sai gidan sarki tana zuwa sashensa aka sanar da ita yana sashen iya ga dare ya tsala Nan da Nan ko tace magana ce muhimmiya idan aka Bari gari ya waye akwai matsala duk ta kwashe komai ta gayawa masu tsaron fada harda guduwar su Tenkwai ai da gudu sukayi sashen iya kaho na gab da fadawa rijiya iya ko kamar ta mutu Dan bakin ciki Banda wari ba abunda yakeyi ga shegen datti sai Jin Kiran Gaggawa yayi daga bakin kofa da sauri ya Mike Rai bace Dan an Gama katse Masa Jin Dadi itako godiya Tai ga sabon ubangijinta daya temaketa kaho be Kama nacinsa akanta ba Yana fita aka isar Masa da labari be jira komai ba yasa aje gidan a kamo Masa kowa azo dashi fada zeje gurin badu yanzu

Ya dau hanya sai gurin badu Yana zuwa yai Masa kirari sai ya Fara wani ihu bazan saurareka ba kaho kunci amanar mu sai da aka Gama Barna sannan zakazo Kuma harda danka na cikinka me Shirin Zama sarki sun kashe mun kububuwa ta tabbas bazan kyalesu ba maza ku bisu sunbi ta barauniyar hanya idan kukai azama zaku taddasu Dan ba wani Abu dazan Bari ya daukesu nine ubangijinku Ni kadai zaku bautawa hahahaha ya saki wata dariya dukansu saina Sha jininsu harda danka Kai Kuma zan barka bazan kasheka ba Kai ta mulki har na Kara baka wani Dan daga amaryar dazakai a anan gaba anemi yarinya azo da ita zan aurama godiya nake ubangijina Ina godiya maza ku bisu ku kamonsu a dauresu agana musu azaba da matarka da danka da matar Dan tsohon sarki da yayayensu da wannan Bakon shine yaron Dana gayama hhhhhhhh dif yaji shiru

Jikinsa har rawa yake yazo gari sai lamunde kawai aka tarar nan da Nan yasa akamo Masa ja'e da iya yasa dukansu akaisu kurkuku aita gana musu azaba yaja zuga suka bi barauniyar hanya badu ya rage musu nisan zangon tafiyar Dan Haka nan da Nan suka karasa suna zuwa sukaga

tashin su a mota shine suka juyo su gayawa badu ko akwai matakin dauka gaba daya garin ya hargitse gashi saura kwana hudu bikin shekara Dole su Kara tsaro da shiri

Cikin ikon Allah suka sauka lafiya da gudu yaran suka rungume kakanninsu Dan sun sansu a hoto ita ko haleema asra da ansar ta rungume cike da tausayin su wace wannan granny momy dinku ce wajenta zaku koma ga Yan uwanku suka dinga murna suna tsalle suka rungume juna suna hugging din juna suka shigo mota bayan ansa musu kayansu duka sukayo gida gidansu hajiya suka Fara sauka suka wuni sai dare suka rakasu gidan anyi sauka anyi komai gaba dayansu  har su asra ita dake macece a kusa da dakin haleema dakin ta yake a sama

Anyi sauka a gidan anyi komai kawai farinciki take Dan Sam ranta ba kunci akai akai mafarkin mijinta take Wai Yadawo gareta suna rayuwarsu cikin aminci Amma tare take ganinsu da wata yarinya me kyau Yar budurwa ta rasa gane ma hakan ke nufi Tai addu'oi inta ansa yaran a makarantar su asra komai tare take musu ba bambamci iyayenta sai murna suke suna samata albarka Haka suke rayuwarsu taje Inda ta bunne akwatin ta ta Haka chas ta dakko kayarta Tai murna Tai godiya ga Allah ta bude gwalagwalanta sai sheki suke ta maida kayanta dakin ta Dan tabar wata jaka ta Kara dealing dinta

Cike da tsoro ta kalleshi sai ya basar kamar beji metace ba Kuma yaji dake Dan duniyane sai yai murmushi my love mekike anan itama ta basar nazo wajen afra kawata da mukazo tare muka samu sabani koka manta ok sannu afra suka gaisa dama chanai ki dawo seat dinki Amma ki zamanki anan tunda dama Nan NE ainihin wajenki naji Dadi da kuka shirya da kawarki murmushi kawai sukayi a tare ya koma ya zauna shizata Kai wajen boka hhhhhh lallai batasan waye alhaji malamalai ba a alhaji labaran tasanni zata sanni kwana kusa ayni nafi bokanta hatsabibanci  Haka suka cigaba da hirarsu da kyar afra ta yadda zata rakata Dan taga mekuma zatai tasa a warware

Sun sauka a airport tare suka sakko da alhaji labaran murmushi kawai yake sakarwa Jeddah surprise name alhajina Zaki gani suna zuwa waje taga motar daya siya Mata huwei ihu ta saki ko kunya ta wani rungume shi alhajina ankawo Ina sauran ya sheke da dariya zasu zo NE Amma sai bayan biki ba key dinki Amma abunda nakeso dake ki koma gidanku a ayau Dan

zanzo banasan zuwa gidan ki gidanku nakesan zuwa Kinga ba girmana bane a ganni agidan wani Tom alhajina karka damu sikai sallama taja motar ta sauke afra a gida kowa da kayansa Niki Niki itama ta wuce gidanta Dan diban kayanta tunda alhaji yace baya bukatar taje da komai

Tana zuwa tadinga sakin horn da gudu suka wangale get din suna mamakin waye a wannan hadaddiyar motar tana shiga Tai parking tana zuro kafarta ta saki ihu waye a wannan sashin Naga angyara shi cikin sati biyu da gudu me gadi ya karaso ai hajiya haleema ce gabanta sai daya Fadi haleema uban meya kawota gidana eye Sakatoto yayi Yana kallonta gidan ta Kuma Amma yaja bakinsa ya tsuke Dan bala'in tsoronta suke ji gashi anmusu takara duk abunda zatai Kar Wanda ya tanka Mata kanaji inama magana kamai Dani wata Yar iska bani guri karna bugeka ya matsa mata ya koma da gudunsa a zuciye ta rufe motar ko sashin ta Bata dosa ba tayi sashen haleema tundaga kofarma abar kallo ce dakyar ta iya turawa ta shiga sashenta

Suma ne kawai batai ba ganin haduwar parlour din ga wata kofa dazata sadaka da sashen yaran ta Kara nutsawa parlour din Bata Nan ita Kuma tana sama ta CCTV camera taganta murmushi tayi tace yau zakici ubanki kin kawo kanki ta sakko daga bene a hankali tana sakkowa suka hada ido ihu Jeddah ta saki ganin yadda haleema ta koma danya Shar gata kamar baturiya hassada ta cikata da gudu tayi kanta Dan ubanki me Kika zo yi gidana gidanki gidanki fa Kika ce sake zance gidan mijin mu dai ko Kuma ince gidan yayana nime Yaya uku maza rigis Aiko Kinga minci gida ihu tasa wallahi karya kike haleema nafi karfinki saina kashe ki

Ta kyalkyale da dariya Naga alama har yau Baki hankali ba to Bari ingaya Miki da Dinma ba karfina Kika fi biyayyar aure nayi Amma wallahi yanzu kikai mun hauka saina illataki na Sanja Miki kamanni Ina Wanda kike haukan akansa baya Nan ba'asan inda yake ba Amma ke farinciki kike to wallahi nafi karfinki fice mun asashe annamimiya duk wani asirinki ya Kare ya karye tanajin haka Tai kan haleema da ihu tuni haleema ta riketa Gam ta Fara waska Mata Mari sai ga bakin ta ya Fara jini gefen idonta yai taruwar jini yauzan nuna Miki nima na iya bala'in cewar haleema da har sunje kasa saboda masifa

_Tofa fans shin meze faru a wannan gida kutara a next page Kuyi manage da wannan sai naji

comment dinku Ina godiya da kulawarku agareni nice taku a kullum akoda yaushe_

*Feedyn bash*
[10/23, 2:33 PM] 👯🏻Ummu Subai'a🎭: *🎭ARNAN DAJI🎭*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

_*ASSALAMUALAIKUM MY FANS WANNAN PAGE DIN SADAUKARWANE GA FEEDYN BASH REALLY FANS NAGODE DA KAUNARKU AGARENI TABBAS KU MASOYANA NE NA GASKIYA MASOYANA NA AMANA NAGA AMANA WALLAHI BANDA KAMAR KU INASANKU INA KAUNARKU INA FATAN KO A ALJANNA ALLAH YA KARA HADAMU ALLAH YABAR KAUNA NAGODE DA KULAWA DA ADDU'OIN KU GARENI KUYI YADDA KUKESO DA WANNAN PAGE DIN FANS DIN AMANA*_

*BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM DA SUNAN ALLAH ME RAHMA ME JIN KAI GODIYA TA TABBATA GA ALLAH UBANGIJIN TALIKAI INA KARA GODEWA ALLAH DAYA BANI IKO NAKE MUKU TYPING👏🏻👏🏻👏🏻*

85-90
```

Yau zan nuna Miki Nima inada zuciya Kuma zan nuna Miki shiru shiru ba tsoro bane ta dinga kilarta tazauna akanta dakyar Jeddah ke nishi Dan Allah kiyi hakuri ki kyaleni wallahi bazan karaba kima Kara idan Ni sa'ar kice shegiya me zubin mayu saida ta lugwiy gwiyta ta sannan ta dagata bakinta ya kumbura yai sintim sai kuka take ta mike tana tangadi wallahi Yar talakawa zakisan Ni kikai wa haka daga yau bazaki Kara yiwa wani bama bare Ni kinsan karonmu dake ai

Ta sheke da dariya Wai asiri to ai ko dama kinsan asirinki baya tasiri akaina sai dai shi mijin naki dakika mallake shi Amma badai sadiya ba shima sakacine da addu'oi Kuma na tabbatar yanzu ya hankalta baze Kara ba maza fice a daki shashasha jaka ballagaza maganganun sun Mata daci a ranta idonta ya kumbura hancinta sai zubar jini yake Banda habo ba abunda take ta fice a fusace ma'aikatan sai kallonta suke suna Mata dariya Dan ansanja sababbi Bata sansuba a matukar harzuke ta danna musu ashar kubar wajan dariya suke Mata kawai ba Wanda ya motsa Dan uwarku Bari na dawo wallahi sai kun bar gidan Nan a fusace ta figi motar ta ta fice tana fita haleema ta Kira al-ameen ta zayyane Masa komai da yafaru ransa ya baci yace zezo gidan zuwa dare

Afra ta Kira kawata Dan Allah fito gani a kofar gidanku haba Jeddah daga dawowar mu ko hutawa bami ba wallahi nagaji abune me muhimmanci akwai matsala mayafi kawai ta dakko ta fito har tazo kifar gidan nasu a hadaddiyar motar daba irin ta a Nigeria ta bude tana shiga mezata gani Jeddah ce fuska face face da jini subhahanallah Jeddah accident kike barin mota kikai Koko ya mtsww wane irin barin mota tana magana dakyar ake gane me take fada ba daya Ina cikin masifa ba hatsari nai ba gears ace hatsari nai da wannan abun kinyar tuni ta dau babban titin Zaria tafara bawa haleema labatin abunda ya faru Wai haleema ce Tai Mata wannan

Haba me afra zatai idan Banda dariya dariya take kamar zata mutu cikinta har kullewa yai yanzu Jeddah Kika zauna mace Tai Miki irin wannan bugun hhhhh chan Kinga dama ranar danake guje Miki ranar nadama ranar sakamako yanzu me gari ya waya ki duba kiga yadda kishiyar da Kika azabtar Kika wulakanta Tai Miki yakamata izuwa yanzu ki hankalta balla Mata wata harara tayi Wanda ya hadamu ma Ina yake Ina na aika dashi wallahi sai tabi bayansa Dan

sai tasan Ni taiwa Haka hhhhh ko Kuma kibi bayan shi ba cewar afra harara ta Galla Mata bansan hauka kinsan gobe za'a kawo komai na aure na kuwa hhhhhh lallai ne ta alhaji labaran a Haka har sukaje dai dai indai suke parking suka sauka suka Fara tafiyar kafa

Afra Tasha alwashin ganawa da boka akan karyai wani aiki zata biyashi linkin ba linkin din kudin sunata tafiya gashi jikin Jeddah ya Fara tsami sai suka fara jiyo wani irin wari abun ya Basu mamaki sun rasa warin meye suna dosar wajen warin nakara karuwa sai da suka sa Dan kwalayensu suka toshe hancinsu Amma Ina mugun wari Wanda sai da yasa afra amai Basu hakura ba suka karasa mezasu gani bokane ya mutu ya rube Banda tsutsotsi ba abunda yakeyi bishiyar da yake da bukkarsa komai ya kone wari kawai yake da tsutsotsi a guje suka juya suka bar wajen suna Fita Jeddah ta fadi ta Suma Allah yasa da ruwa a motar ta tuttula Mata ruwa ta farfado Amma ba ta cikin hayyacinta afra tashiga taja motar dake itama ta iya suka dufafo kano

Suna tafe suna wuce wurare a motar gaba daya a firgice su fadeela suke Banda kuka ba abunda suke musamman idan mota ta shiga Rami kuka sike kamar ransu ze fita takaici ya cika suhail sun tsaya a gidan Mai zasu ci abinci susha ruwa habawa kallon kallo ake tsakaninsu da mutane suhail ya daka musu tsawa suka koma ciki bakin kamar zasu mutu aka siyo musu indomie Nan fa yasha takaici

_To fans Bari indaka anan Kuyi manage da wannan wallahi fans saboda kaunarku agareni nayi wannan typing din NAGODE da kulawa nice taku a kullum a Koda yaushe_

*Feedyn bash*
[10/23, 2:33 PM] 👯🏻Ummu Subai'a🎭: *🎭ARNAN DAJI🎭*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*Assalamu alaikum my kawa tagari Wannan page din sadaukarwane agareki my ameeneeya ta Amana  fadeela takwarar tenkwai🤣🤣 saboda kaunar danake Miki yasa nasawa Tenkwai sunanki Allah ya albarkaci rayuwar mufaddal dina👏🏻👏🏻 inasanki har Raina sister Allah ya bar kauna kawata ki shafamun kan Dana kice ya Fara siyan kayan kaninsa ko kanwarsa 🤣🤣🤣wannan page din nakine*

*BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM DA SUNAN ALLAH ME RAHMA ME JIN KAI*

90-95

Na suka Fara ihu wayyo tsutsa a a tanace su wallahi bazasu ciba ihu suke suna kuka taikaici ya gama cikamasa ciki ya daka musu tsawa baku da hankali ne angaya muku Nan ma daji ne dazakuyi mun hauka KE fadeela kinfi kowa iskanci ku shiga hankalinku fa haba kamar ya Kara tunzurasu ihu fadeela ta saka ka dakkomu zaka kashe mu wallahi bazamu ci wannan ba cikin ikon Allah sai ga me doya da miyar alayyahu dama suna noman doya cike da murna sukace zasuci aka sauke musu sukaci suka Sha ruwa sukai nak mutane Banda dariya ba abunda suke musu wannan Abu Haka tashin hanakali fada Dame gari ranar sallah Nan suka dau hanya zuwa Kano
```

Direct gidan kawu suka wuce Wanda tuni yabawa suhail kan motar saboda tsabar haukan dasuke da kauyanci duk abunda suka gani sai sunyi ihu ko dariya gaba daya sunzama kamar mahaukata Rama ce ta fashe da kuka gaskiya yaya suhail ka cucemu dama Haka ake rayuwa a duniya kaki kazo kadauke mu tuntuni to da tuni muna chan muna Shirin dibgar Roman shekara shi dai kawu dariya kawai yakeyi sai bayan sun shiga Kano suka nufi gidansa dake sharada Nan suka yada zango dakyar suka shiga gidan Dan Basu taba ganin gini irin saba danma suhail yayi musu bayanin yadda garin yake a hanya

Gidanta suka je lokacin karfe takwas na dare suna zuwa tayi parking ta kamo Jeddah sukai bangaren ta ko Ina a gyare ta kwantar da ita chan sai ga Al ameen Yana zuwa ya doka Mata harara to Yar iska kingama yawon tazubar din naki wallahi yau sai kinbar gidannan tunda bana ubanki bane ba sisin ki a ginin gidannan azafafe ta mike ya isheka Al ameen a yanzu ko zanbar gidannan tuni ta Fara hada kayanta ta dakko duk wani abunda zata bukata kozaka ban wuri murmushi yai Mata Amma na mugunta Yana fita ta Fara daga katifa abun mamaki duk wani abubuwa nata na asiri Babu su ihu ta dinga zindimawa kamar mahaukaciya

Afra dariyace ta subuce Mata na shiga uku afra kidena dariya Ina neman kayan asirina ne da boka yaban mutum mutumin zan maida zuciyarsa ga alhaji labaran hmm lallai Jeddah har yanzu Baki saduda ba wallahi tun da Naga yadda gawar boka ta wulakanta na Kara tsorata da lamarin rayuwa ki hakura kibi Allah mtsww dallah chan gafara zan tuba NE Amma ba yanzu ba saina tatike alhaji labaran Haka suka fito ranta a bace harda envelope dinta ta takaddun gidan suhail da duk wata kadara tashi Bata San ansaja ba ansa Mata na bogi suka wuce tana hararar Al ameen Dan shi take zargi Bata San komai na asirin ta ankwakule ba shashasha Allah ya shirya

Haka suka koma gidansu tana shiga gidan wani gululun bakin ciki ya tokareta saboda wani Baki da gidan yai ga wani mugun wari suna shiga sukaga ummanta a kwance gabanta duk ya rube sai tsutsotsi yake  rufe hancinsu sukai gaba dayansu hankalinsu ya tashi lafiya umma meya sameki cewar afra data karasa gareta Amma jeddah tsaki taja ta koma waje gaskiya bazata iya zama a wannan gidan ba tasan me zatai zata nemi hotel ta Kama na two weeks tanemi iyaye

na bogi su daura Mata aure a hada Mata na karya a karbi lefe abunda ta tsara kenan aranta Bata bi ta kansu ba ta fita taja motar ta Tai gaba

afra kitemakeni Banda lafiya tun Ina zuwa asibiti Abu yaci tura inata boyewa ne Amma na kamu da cutar daji wadda kukewa lakabi da cancer yanzu Haka tanga ne ya kaini asibiti akace kudin aiki dubu 700 Kuma nasan Yana da ita Amma yace be da ita ya kawoni Nan ya yasar har yau ban Kara ganinsa ba kitemakeni afra cike da tausayi tace Ni Banda kudi a yanzu Dan bikina saura sati daya Amma bara na Kira jeddah tana fita taga wayam ta duba dakinta Bata Nan bandaki ba kowa ta leka waje wayam ba motar ta ta gudu kenan itada uwarta bare ni tuni itama ta karawa kafarta burki ta tafi gida itama tana Allah wadai dasu jeddah insha Allah alakarsu ta yanke tana tafiya sai ga text dinta ya shigo idan kingaji Kya tafi ki kyaleta kwashe kwashen ta na masifa taje wani yai Mata cin dayafi karfinta ya rubata Dan Haka ki kyaleta Naga uban daze Kara cinta a Haka tunda ita batasan ta girma ba Tofa lallai wayannan Basu da mutunci cewar afra tuni tasa number dinta a divert

Jeddah Bata zame ko Ina ba sai gidan wata dillaliya a Yan lemo Tai Mata bayanin komai ta amince akan kudi dubu dari biyu sunyanke maza za'a nema su karbi lefe su daura aure Baki alaikum haka ko akai ansamu wasu dattijan biri zauna gari banza aka tsadance su uku ta Kira alhaji labaran ta Gaya Masa komai dariya kawai yai ba matsala gobe karfe goma na safe zasuzo su kawo Haka ko akai washe gari ta Kama asabar aka kawo kayan lefe akwati Sha biyu sai kace wata budurwa budurwar ma ta yayan gata da sadaki dubu dari biyu da kudin gaisuwar iyaye dubu dari uku gaba daya dari biyar suka kawo murna kamar jeddah ta zuba ruwa a kasa Tasha daya tambayeta meyasa aka kawo Nan bayan da tace a dangwauro take sai ta waske kawai

Ai chan din babanta dama ya mutu mamanta Kuma Bata garin sunyi waya tace azo Nan gidan kanwarta Haka suka bar maganar bayan sati daya akai bikin afra aka kaita me Dile batai party ko daya ba sai dinner da ango yai bayan daurin aure an kaita gidanta suka Sha dinner dinsu tadai yi walima agidansu anyi biki lafiya angama lafiya duk wata kawa datasan ta barikice Bata gayyaceta ba iya Yan unguwar sune da Yan uwanta matar babanta bataso Tai wannan auren ba bakin ciki kamar tayime gashi ta samu mijin marainiya akwati takwas yai Mata komai Masha Allah sai muce amarya Allah ya bada zaman lafiya

Haka jeddah tadinga shirye shiryen ta tsaf dangane da nata bikin tasha gyaran jiki tayi kyau dama jikinta me kyau ne sai ta dawo tamkar wata fure Dan kyau tayi fes abunta gwanin Sha'awa biki ya rage saura kwana uku duk wasu fitinannun kawayenta ta gayyacesu Dan party suka shirya har kala biyar zasu watsu su lalace ya bude Mata bakin aljihu sai bindim bindim take a ciki gashi komai ya sauke mata na daki tasan ita me sa'a ce a rayuwarta bazata taba auren wahala ba wata kawarta ta hadata da wani  hatsabihin boka megani har hanji yagama shiryata yadda zata tunkari gidan alhaji labaran Tofa  maji magani jeddah koza a Kara dacewa

_*To fans sai naji comment dinku gaskiya na yanke shawarar Dena posting kowane book nawa a wasu groups din sai nawa Dan bakwa mun comment wahar dakaina kawai nake iya fans Dina kemun comment wallahi indai Banga sanji ba daga yau nadena posting din book Dina a kowane group nice taku a kullum a Koda yaushe*_

*Feedyn bash*
[10/23, 2:33 PM] 👯🏻Ummu Subai'a🎭: *🎭ARNAN DAJI🎭*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*Assalamu alaikum my fans inafatan Kuna lafiya Dan Allah kuyi hakuri na rashin jina kwana biyu
```

hakan ya farune sakamakon rashin lafiyar danake fama da ita kuyi hakuri kumin uziri ba kullum zan dinga muku typing ba Dan Allah kudinga kokari Kuna posting zuwa wasu groups din wallahi bazan iyaba abun dayawa nagode my fans nagode da kaunarku a gareni da tarin addu'oi in da kuke mun suke Kara bani karfin gwiywar faran ta muku kamar yadda bakwa gajiya dayimun addua akara hakuri dai dani👏🏻👏🏻👏🏻👏🏻*

95-100

Jeddah duk wani shirye shirye ta Gama tayi gyara na tashin hankali ko budurwa albarka har wani yalo yalo take wankan inji akai Mata jikin ta yayi smooth ga alhaji labaran ya sakar Mata bakin aljihu facaka kawai take da kudi ta tattaro ta dawo gidan hafsa dillaliya hankalinsu kwance suke shirye shiryen biki wadda hafsa ta Zama uwar amarya ga wayanda aka debo haya a matsayin iyayen ta maza tunda dama mahaifinta ya mutu a matsayin abokans da Dan uwansa suke Tayo gayya ta manyan Mata matan dasuka amsa sunansu Mata wasu zawarawa ne wasu matan aure wayanda suka gagari mazajensu wayanda suke haduwa a shargallensu yammata ma ba'a barsu a baya ba bikine ta shirya shi nakece raini anshirya karya a bikin ko dayake da abun ai

Kawarta ce ta rakata gun boka sangamu ya Bata lakanunnuka da magungunan dazata mallake mijin ita kadai ta juyashi San ranta sannan ya Bata Wanda zata haukata haleema saboda bala'in haushin dukan datai Mata ya Bata Amma sai yai wata wata daya yake Fara aiki sannnan ya Bata  Wanda zata kashe yayan Amma da sharadin indai aka kuskure wani ya ganta sanda take aikin ita zata haukace Kuma a haukan zata mutu ba magani ta yarda da hakan gears yaran su mutu nata su tsira ai ko tana tafiya Bata zame ko Ina ba sai gidansu ita da haleema ta Gama shirya duk wani plan ita da kwayenta ta ajiye su a hanya ta danna horn megadi ya bude Mata direct part din haleema tayi

Tana shiga ta tayi nocking aka bude Mata sannan ta zauna haleema ta hade fuska tan jiran Taji taima ta wani haukan na daban ko zancen banza Amma sai taga ta durkusa kasa tana hawaye kiyi hkr Yar uwata da duk abunda nai Miki ki ya femun nazo neman gafararki dama bikina za ai na kawo Miki iv nazo na Gaya Miki na nemi gafararki gaban haleema yai wani irin faduwa ta ringa addu'oi a ranta tana rokon Allah ya kareta daga sharrin Jeddah idan da wani mugun abun tazo Allah ya maida Mata da kayanta kanta ba komai na yafe Miki jeddah cike da farin ciki sai washe Baki take nagode sosai Yar uwata Nan suka dinga kwasar Hira Amma Jeddah Anya ko

Baki garajan daura aure ba baku da tabbacin mutuwar suhail fa dariya tayi haba sadiya inbanda abinki suhail ai ya Dade da mutuwa shekara kusan daya ba amo ba labari ai Dole mu fidda Rai Kuma anga takalmansa a wajen da hularsa to shi Yana Ina har zaman makoki anyi Masa fa Kuma ai nayi takaba ko haleema dai kallonta take cike da mamaki ai kema kawai ki auranki Dan Kinga gaskiya da kyanki gwara ki Mori lokacin ki ki auren ki kema

Shiru kawai Tai Mata tana ta nazari chan Jeddah tace haleema Baki da abinci ne Tai murmushi Yana cooler a flask naci nawa saura na Yara debo kici to tace ta nufi kitchen din maryama ta koma bangaren haleema dama tunda Jeddah tabar gidan Al ameen yai Mata korar Kare tunda ta shigo tana jinta tana bayan kitchen tana wanke wanke ta Gama Kuma Tai zamanta bataso su hadu Sam Dan tanajin tsanarta fiye da yadda haleema ke tsanarta ta shiga kitchen din harda cire mayafi haleema Bata kawo komai ba ta debo hadaddiyar jelop din shinkafa taji kayan lambu da nusashshen kifi ta zuba a plate maryama na hangota tana ta mamaki kodai da gaske ta sauta

Ta bude freezer ta dakko drinks me sanyi ta duba ba kowa dake hangota ta warware zaninta ta kwanto maganin yaran ta barbada musu a ciki tana karkade hannunta maryama ta Kara lekowa Bata ga komai ba Amma jikinta ya Bata wani abun ta zuba ta dakko abincin ta dawo parlour tanata zurawa sunata hirarsu kamar gaske sai da taci Tai Kat Tai Mata sallama ta fito zata rakota ta hanata itako Maryama Sam hankalinta be kwanta da zuwan Jeddah gidan ba bataga dai me ta zuba ba Amma tabbas tayi wani abun tana Nan tana jiran ta tafi bacci me nauyi ya dauketa a wajen dama wajene me kyau

Tana fita ta fito da maganin da akace idan dai halima ta shaki kamshin sa zata haukace ta fef fesa shi yadda ze shiga wajenta abun tsautsayi me wanki yazo kawo kayan wanki ya ganta tuni ya kunshe bakinsa ya juya Dan shi tsoronta yake ba ruwansa Haka ta ja motar ta Tai gaba cike da murna tana fita direba na sako hancin motar yaran suka fito ansar ya taho da gudu ya fada kan haleema momy abinci to Dan gidan momy autan momy bara na zubo ma ta mike taje ta zubo masa Nan ya Fara cin abincin magriba tayi Jin Ana kwalla Kiran sallah firgigit maryama ta tashi ta shigo gidan da gudu taga yaran duk suna parlour ansar na cin abinci da sauri ta karbe ya saka ihu Yana Kiran momy

Lafiya waya taban autana cewar haleema ranki ya Dade nice banyarda da abincin bane Allah yasa ba Wanda yaci no ba Wanda yaci menene wato hajiya Ina taga Naga kamar maman asra tasa wani Abu a abincin to Kuma bacci ya daukeni kafin nazo na dauke na zubar ikon Allah wallahi dama sam banyar da da itaba maza jeki zubar shi Kuma insha Allah ba abunda ze same shi nasan dama Dan Ni da yayana tayi ba yayanta ba Dan ba yarda za ai taima yayanta Haka ko akai ta zubar ta Dora musu indomie suna ta Kiran abinci cikin 10 minutes ta kawo musu suka ci hankali kwance sunata hirarsu hankali kwance suna Al ajabin Hali irin na jeddah tunda duk cikinsu ba Wanda take bakon sa

Jeddah ta cika da farinciki aikin ta yayi batasan yayanta suna hannun haleema batasan Dana nata yayan ba ta dauka suna gurin hajiya shiyasa idan zaka Gina Ramin mugunta Gina shi gajere Dan karya fada dakai Haka ta koma gidan hajiya hafsa tayi yadda boka yace Mata na zubawa a abinci duk ta ajiye na cushe cushe duk ta tusa tayi kyau kyan Dan miciji idan Kika ga Jeddah tamkar fure angama komai an na biki anfara biki anyi shagali iya shagli anyi lunch anyi party ya ake dinner a Bristol palace guri yayi guri Mata masu ji da kansu sun hadu maza sugar Daddy masu ji da kudi sun hallara matane manyan Mata matan aure wayanda suka gagari mazajensu da zawarawa wayanda suka gagari gidansu da yammata wayanda suka gagari iyayensu matan bariki manyan alhazawa ne ke ta faka manyan motocinsu Nan aka Fara dinner anci an Sha

Anyi wadaka da nera amarya ta samu kyaututtuka daga hannun abokan ango ta samu kyautar gidaje da motoci da makudan kudade ita kanta abun ya daga Mata hankali soboda Bata taba ganin amaryar da akaiwa kyauta ranar bikinta ba kamar ta mahassada hassada ta cika musu ciki masu kaunarta kodan su rabe ta su dangwali arziki sunyi murna ance arziki kashi tofa Jeddah ta tako shi me shegen wari inji wasu kenan ba wani Abu daya daga hankalin jeddah ganin yadda taga maza na hugging din juna manya masu ji da kudi masu mataye da yayaye a gida amma sai Ta basar ba abunda yafi Bata mamaki irin yadda Taji Ana ambatar mijinta da malamalai na duwai kowa Haka yake cewa chan sai ga alhaji duwai ya bayyana hankalin ta be idda tashi ba sai da taga alhaji malamalai Yama manta da ita ya rungume duwai har dasu kiss Nan aka Fara sabuwar chashewa aka Fara budiri Nan taga Ana kawo kwalabe ta tabbatar giyace su kuma matan aka dinga hadasu da shamfen anci ansha anyi shagali

Ba a tashina sai karfe daya anan aka Kama dakuna Mata ganin yadda akaiwa jeddah Nan suka

Fara sake salon iskancin Taku ko wacce da kalar nata upwayanda ke neman Mata suka Fara kamu masu neman junansu ko suka shige daki Dan wasu sun maku a cikinsu Haka ko akai alhaji labaran ya lallabata suka shiga daki da sauran kawayen su da basi kasuwa wasu da dama sun gane Dan homo zata aura Amma ba halin fada Haka suka shiga dakin sunata Hira suna Tai Mata famfo Akan karta yarda ta zauna da kishiyoyi Dan ta Zama hamshakiyar hajiya yanzu shiko alhaji malamalai nachan da alhaji duwai sunata buga Masha'arsu Dan an Dade ba'a haduba tun kafin ya tafi Dubai Basu bar Juna ba sai gab da asuba ragowar ma Haka suka dinga barzar junansu Jeddah tana complain din yadda suke rungume rungume sai kawayenta suka nuna Mata tsabar wayewace da zaman turai suma ba Haka sukewa junansu ba ta yarda a Haka hankalinta ya kwanta

Asubar fari Ta mike ta Fara shiri ko ta kansu Bata bi ba ta fice Dan Shirin daurin aure taje gidan hajiya hafsa karfe takwas ta tafi kwalliya goma dot ta dawo tayi kyau kamar Yar tsana tamakar fure an daura auren alhaji labaran da hajiya hafsa sadakinta dubu dari biyar lakadan Ba ajalan ba andanyi chasu a green park sunci sun Sha karfe shida aka kawo motocin Kai amarya kowa ya samu Yan gulma da Yan bani na iya Kai tsaye sashenta aka kainta Yan ganin gida sun Gama gani dama ba dnginta ko guda hajiya hafsa ce ta tarasu tace Yar yarta ce wasuma sun dauka budurwace Dan jikinta me kyaune bakace Tama taba haihuwa ba

Bayan kowa ya tafi ta mike ta zagaye sashen nata tsaf bala'i gida yayi gida Bata iya ganin sashen nata ba ta koma ta rufe fuska koma zata rufe oho taci kwalliya tayi kyau chan Taji hayaniya ta dauka abokan angone harda gyara Zama Nan aka Fara nocking Tai shiru tana jiran ya shigo da karfi Taji an hankado kofar Ana zage zage ke Dan uwarki kinaji muna bugu Baki bude ba dayar ce ta janye mayafin eh lallai wannan kyau haka ga kwalliya duk a gidan Nan to daga yau Zaki dau darasi Dan uwarki matane manya su biyu da yammata uku ko wacce rike da zabga zabgan bulalai keba kwadayi Yasa Kika aurar Mana Miji ba wallahi na lahira sai ya fiki Jin Dadi zakisan kin shigo gonarmu suwaye ku cewar Jeddah Bata rufe Baki Taji an waska Mata Mari tana dagowa aka Kara Mata ta saki wani ihu momy ta matso ta daki bakinta sai da ta cire Mata hakori ihu ta saki na azaba

Ku daketa kuyi Mata dukan mutuwa tamu sannu da zuwar kenan tunda Baki da mutuncin daza a kawoki ki gaishemu Nan suka zage balaga sukai Mata lilis Tana ihu tana komai Amma ba Wanda ya daga Mata kafa sai da ta daku sukaga da kyar take motsi suka fice suka barta a yashe face face cikin jini cikin kukan ma ta gagara yinsa Nan da Nan fuska Tai him ko Ina jikinta

ciwo yake jitai anturo kofar da karfi bakaramin firgita Tai ba

_To fans Bari mu kwana anan sai zuwa gobe insha Allah koya Labarin su ja'e sai gobe zamu leka musulman daji muga halin dasuke ciki akara hakuri dani😂😂😂yanayin jikina ne sai a slow nice taku har kullum a Koda yaushe_

*Feedyn bash*
[10/23, 2:33 PM] 👯🏻Ummu Subai'a🎭: *🎭ARNAN DAJI🎭*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*_~Assalamualaikum masoyana bazan gaji da godiya agareku ba fans musamman feedyn bash real fans da kainuwa fans da komai mukaddarine fans da matan aljanna Ina Jin dadin yadda kuke nuna min kauna bakina baze iya furta adadin kaunata agareku ba hannuna baze iya rubuta sakon godiya a gareku ba Sai dai nace Allah ya biyaku da gidan aljanna nagode da addu'oin ku agareni nagode nagode nice taku kullum a Koda yaushe maman yan.......kundai gane beauty😂😂😂😂😂~_*

*Bismillahir rahmanir Raheem da sunan Allah me rahma me Jin Kai*
```

*Book 2*

100-105

Alhaji labaran ne ransa a mutukar bace ya bude kofar da karfi Yana zuwa ya dauke Jeddah da mari Wanda sai da taga wuta Dan ubanki su hajiya sa anninkine daza a kawo ki baza a kaimusu ke ki gaishesu ba suna gaba dake to wallahi idan kinasan kanki da arziki ki musu biyayya yi nayi bari na Bari Dan dasu Zaki zauna a gidan Ni idan nasa kaima sai kin ganni ba'a wulakanta mun iyalai na bazan dauka ba fada yake kamar xe Ari Baki Jeddah da take kuka kamar ranta ze fita na shiga uku Ni Jeddah yau Kuma gidan danazo Kenan Ni za'a yiwa duka a Daren aurena zancen da take Kenan a zuciyarta tana ta kuka mtsww dadine yai Miki yawa Ni Zaki tasa agaba kinawa kuka ubanme akai Miki Dan wannan Marin danai Miki ai shafar Mai ne dago fuskarta Tai jage jage da jini da majina ga jikin ta duk yai tsami

Habawa wata muguwar dariya alhaji labaran ya saka wadda har durkushe wa yai Dan mugunta a'a amarya me ya sameki haka a fuska ta bude Baki zatai magana sai ga wawulo habawa wani muguwar dariya yasa harda dukan wardrobe amarya me ya faru barin mota kuka yi koko me nidai ba'a cemun anyi hatsari ba to anyi hatsari ai da tuni Kuna asibiti ma meya faru gayan inji ta Kara rushewa da kuka wallahi sai ka sakeni a Daren Nan wallahi bazan zauna dakai ba matan ka da yayansu suka hadu sukai mun wannan dukan nacin mutunci niba jaka bace Kuma ba baiwar su bace sakina zakai

Yana Jin haka ya sakko ya rungumeta ya Fara lallabata haba beka mata kina fadar haka ba zan musu magana karsu Kara dukan ki banasan duka ke Kika Bata musu Rai shiyasa ganin Yana lallabata tuni girman kanta ya motsa ta Fara bala'i bansan Kai lusari bane sai yanzu dama Tsoron matan ka kake ka auroni wallahi basu daki banza ba bazan yarda ba ehe niba jaka bace gobe zan debo musu police su kamama munsu a bimin hakkina be Bari ta karasa magar ba ya hankade ta kanta ya daku gado dama kasa suke Nan da Nan yai wani malolo be dai fashe ba

ya dinga kifa mata Mari hakan be Masa ba sai daya fito Yana huci ya shigo da belt ya dinga laftar ta tun tana ihu har ta Dena Ashe Suma Tai

Gaskiya na tausayawa jeddah Dan ta daku ga dukan iyalan sa ga nasa sai da ya gaji Dan kansa ya Yar da belt din ya zauna Yana maida numfashi ransa ya baci yasan ta daku Amma baze barta ba yadda yasha magungu na baze iya daga Mata kafa ba tashi malama zami magana shiru tashi nace ba magana Yana tabata yaga ta bingile ihu tasa no karki mutu Dan Allah bangama amfana dake ba ba auren ki naiba siyanki nai Dan haka dole na amfana dake da gudu ya nufi fridge ya dakko ruwa me mugun sanyi har ya Fara kankara ya Fara tsilala Mata

Wata ajiyar zuciya ta saki jikinsa na rawa ya fara tabata sannu Jeddah kiyi hakuri lefinkine wallahi yazaki dinga gayamun maganganu San ranki karki Kara gaskiya kawai binsa take da ido taba shi tausayi dan ta daku ya dauketa ya cika baf da ruwa me Dumi yasata ciki ya gasa Mata jikin ta yai Mata wanka tas ya nadota jikin ta ya zige da zazzabi sai karkarwa take Nan da Nan ya Bata magani tasha ya kwantar da ita Yama hakura yau ze kyaleta saboda yasamu cikar burinsa Amma me sai wayarsa ta Fara kida Yana dubawa yaga ansa my duwai da sauri ya daga Yana fita daga dakin hello my ykk iceko ka Fara aikin kasan sai Kai sati biyu kana yi sannan Kuma Dole ka dauke duk wani tausayi cikin wannan aikin na sha'afa sosai nagode my duwai ya kashe wayar ya hade fuska ya koma dakin harta Fara bacci Yana shiga ya dala Mata duka a firgice ta farka lafiya murmushi yai Mata hakkina Zaki bani

Tasan bashi da imani tuni ta Fara hawaye Banda lafiya bazan itaba Zaki ban ko saina saye Miki karfi ganin ya nufo ta gadan gadan yasa ta gyara Amma sai yace goho zakimun bazan iya ba alhaji mutuwa zanyi to ki mutu Mana banza kawai ya juyata tana ta hawaye Amma me sai ji Tai ya dumfari dubura ba a wajen kasa ba alhaji nafiki sani ai anan nake so Nan nake ci ni bancin tsuliya niba rago bane namiji ne Ni haba Yana Fara kokarin sawa ta saki wani ihu habawa be sauraretaba yasa karfin sa ya danna sai jini habawa tuni jeddah ta sume Nan ya Fara gwatso yanayi Yana ihu Yana wani irin kuka kamar saniya har wani tsalle yake itako Jeddah Bata hayyacinta a sume take Yana kawowa yake komawa sai karfe hudu ya kyaleta badan maganin ya sake Shi ba Yana juyata yaga Bata numfashi hhhhhh shegiya Jeddah duniya Wai kece ke Suma koda yake kindan ban tausayi Dan nasan dama nikan su hajiya ta ba wasa Kuma kikai min left na Kara Miki bara ma temakeki ki dawo hayyacin ki ya Mike ya dakko wani ruwan ya zuba Mata ta zabura tana wani irin mimmikewa

Kobi takanta beba sai bacci da kyar taja jiki duk face face da jini ta shiga bandaki ta Tara ruwa tana ta kuka da nadama Ashe irin gidan data shigo Kenan tausayin suhail fal ranta Allah ya yafemun tofa chab lallai Jeddah ta shiga ruwan ta saki wani ihu daya tada alhaji ya leke a firgice yaga ta Kara sumewa mtsww ita Kuma wannan Suma bayai Mata wahala  mtsww Ina baccina me Dadi kin tasheni Ina mafarkin duwai Dina yadda nake sukuwa akansa mtsww ya shiga ya temaka ya watsa Mata ruwa ta dawo normal ya fito ya barta tana ta kuka ga radadin dake damun ta Ina zata Sanya rayuwarta ita yanzu ga gidan cike yake da tsaro ba damar gudu kuka take Mara sauti a bayin

Haka ta Gama ta rarrafoo ta fito har an Fara Kiran sallar asuba a lokacin ta fito ta jawo rigarta ta zura so take ta gudu taje ta wajen boka a daukar Mata mugun mataki akan wayan Nan mutane ta bude kofa a hankali ta dauki key din motar ta ta fice amma me tana zuwa get taga wasu tankama tankaman mutane tayi tayi su barta ta fita sunki ga jikinta duk ciwo yake fuskarta ta kumbura ko idon ta ba'a gani asibiti zanje Banda lafiya sukansu sunyi mamakin ganin tace itace amaryar gidan gata a kumbure kodai har ta Fara gamuwa da fushin su hajiya ne suka hanta fita fafur saboda alhaji yai musu mugun takara ganin ta fito daga motar yasa suka firgita da yadda jikin nata yayi Nan da Nan sukai ta Kiran wayar alhaji akashe sukai shahada suka Kira ta hajiya bugu daya ta daga cike da magagi

Cike da magagi waye nan suka Gaya Mata amarya ce ta fito ba lafiya Kuma alhaji yace kar abarta ta fita kan uba gidan ubanta zata tuni ta watstsake gani Nan zuwa ta fito a fusace taja Jeddah tana kuka tana ihu ga jiki duk ciwo Amma bame ceton ta sai da ta kaita har side din ta tana ihu tana komai ba Wanda yasan tanayi saboda girman gidan da girman bangaren nata Nan ta dinga kilarta kamar ta samu jaka ta wuce fuu sai gata da tulin kayan wanki Dan ubanki Fara Kuma wallahi idan Basu fita ba sai kin Tisa kigama kiyi Mana girki suma ne kawai batai ba tana ji tana gani ta Fara wankin

Sarki kaho ne yake wani irin ihu yasa an kamo Masa ja'e da iya da lamunde yasa aka yi musu bulala dari dari gaba dayansu sai da suka Suma Nan yasa aka daukesu dukan su aka kaisu kurkuku ta karkashin kasa yace Kar a Basu komai Koda ko ruwa ne har sai sun Fadi inda su Tenkwai suke iya da lamunde sunfi jikata Dan sune Mata kaho kullum cikin shan burkutu yake

ransa ya gama baci hankalins a tashe yake gefe guda Kuma Ana ta Shirin bikin shekara ba abunda aka fasa anata kiwata mazan daza a yanka

To fans gaskiya comment yayi sanyi fa wai yane ko littafin yadena dadine gashi ya kusa karewa befi saura five pages ba inama kowa fatan alkhairi nice Taku a kullum a Koda yaushe

*Feedyn bash*
[10/23, 2:33 PM] 👯🏻Ummu Subai'a🎭: *🎭ARNAN DAJI🎭*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

_*Assalamu alaikum wannan page din sadaukarwane agareki my sister queen Indo marubuciya aljana Aisha now typing Yan uku I love you Lodi Lodi inayinki irin eh irin sosai din Allah ya Kara basira da fasaha da juriyar typing da kwarin eyes ki dade ki lastin sister allah ya kawo miji nagari haihuwar fari kema ki zandaro yan uku allah ya kara fasaha da juriyar typing adinga suburbudo mana yan uku kullum 🤣🤣🤣🤣*_
```

*BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM DA SUNAN ALLAH ME RAHMA ME JIN KAI*

*Book 2*

105-110

Yadda ki kisan ana kiwata shanu haka ake kiwata mazan da za'a yanka wannan shekarar abinci ake loda musu kamar hauka suna ci suna amai haka ake basu sunyi jibga jibga dasu jini yana gudana sosai a jikinsu yadda badu ze sha jini ya koshi shiri ake bana wasa ba dan aranar za'a yanka su ja'e suma umarnin badu ne wannan in banda kace nace ba abunda ake agarin hakan ya kara tunzura iyalan ja'e suka sha alwashin rike addinin da ja'e ya basu dan suna da tabbacin shine gaskiya

Banda azaba ba abunda ake gana musu baci ba sha inda aka kaisu kar kashin kasa ne ko mikewa baka iyayi bare ka kwanta a tsune suke bacci sai dai barawo saboda ukuba duk kansu ba wanda be suma ba haka suka fita hayyacinsu suna barazanar mutuwa da ba shiri aka aika agayawa sarki zafa su mutu dan lamunde a ranar sumanta takwas iya ce me biyar ja'e biyu ba ci ba sha tsawon kwana hudu gashi sunki suce komai tun suna fitsari da kashi har sun dena hankalin kaho ya tashi dan badu be ce ya kashesu ba jinin su yake so ya sha da hanzari ya tafi kurkukun da kansa

Yasa aka fito dasu ya basu abinci da ruwa har sun fara dawowa hayyacinsu duk da abincin ba me dadi bane ya kallesu cike da tsana ke matata dake za'a ci amana ta koda yake dan cikina ma har dashi anya ko ba sanja mun da kikai ba ta doka masa harara kamanta sanda ka kashe mun iyayena a gabana wallahi kaho allah ubangijin musulunci baze barka ba sai ya kawo karshen zaluncin ka da temakon suhail ya daga hannu ya dalla mata mari wanda sai da hancin ta ya fashe yana wani irin huci ba wani ubangiji sai badu kuma yadda na hallaka iyayenki kema zaki bisu dan bazan barki ba dole ki mutu ya hankadeta ya dallawa lamunde harara ya jawota gabansa zakigaya mun waye wannan yaron kose na datse miki hannu yanzu

Tayi murmushi koda zaka kasheni nadena numfashi allah yana tare dani alhamdulillah nasan shahada nayi kuma yayana bazasu barka ba zasu daukar mun fansa ko yanzu burina ya cika dana ya dawo kasarsa ze sauke ka ya kawar da zaluncin ka ya kasheka kamar yadda babanka ya kashe kakanninsa kai kuma ka kashe mahaifinsa wata muguwar kara ya saki yada takobi ya sare tsintsiyar hannunta tasa ihu ta fadi a sume rikicif ganin gaka iya ta kara fashewa da kuka saura ke zan fada zan fada tana kuka ta bashi labari tundaga zuwan suhail har tafiyarsa

Shakota yai yadinga dukanta munafika na tsaneki dama ashe bakya kaunata kika ajiyemun bako a gidana da kyar fadawan sa suka karbeta badu ya temake ka kace badu zakaiwa kyautar jininsu dan haka karka kashe su kuma tun yanzu wata ajiyar zuciya yake yana wani jan numfashi ku maidasu haka aka kwashe su kamar wanki aka maidasu inda suke adinga basu abinci so daya ruwa so biyu saura kwana biyar bikin shekara yau dan haka a tsananta tsaro a garin nan

Haka aka zuba fadawa ta ko ina a garin harda mata bayi tundaga farkon daji har cikin gari anan suke kwana saboda  tsananin tsaron da aka sa a garin zuciyar kaho kamar zata fashe ya gama sanin sirrin garinsa gashi ya gudu da yammatan dan angaya masa da Rama kadai ze samu haihuwa a yanzu amma dole ya nemeta saboda idan ya kashe su ja'e ta haifa masa magaji gaba daya garin kuguru yana cikin mugun tsaro hankalin kowa a tashe yake sun dauka yaki za'ai duk wajen bokan da kaho zeje a garin sai ace da Rama kadai ze iya haihuwa gashi badu yace ranar bikin shekara yazo da budurwar datai masa gaba daya yana cikin tashin hankali

Su suhail sun huta matar uncle dakanta taja su fadeela tayi musu wanka kamar jarirai har amai tai saboda datti ga wani hamami dasuke ta Kara yi musu wankan tsarki tazo kan subai'a kuka tasaka ganin yadda gabanta ya jagale Nan ta hada ruwan Dumi tasa gishiri da Dettol ta cika ruwa a baf tasa ta take tasaki wani ihu sai da Tai suman hucin gadi tafi Rabin awa a ruwan sannan ta cireta Tai Mata wanka taji dadin jikinta sosai dakanta ta fito daga bandakin Nan tasamusu dogayen riguna sunyi kyau abunsu ba abunda suka iya a duniya kamar jarirai sabuwar haihuwa tausayinsune ya lullubeta dama akwai irin wayannan a duniya wallahi ta dauka sai a TV wayannan bazasu taba wayewa duka ba saboda fadar annabine Dan kauye sai ya shekara arba'in a birni yake wayewa Aiko sai dai addu'a wayannan

Suhail ya nemi izinin tafiya gida Nan uncle yace shize Kai su Amma matarsa fafur tace a bar Mata su fadeela beso ba Amma ya roki alfarmar su tafi su gaida su daddy sai dawo ta yarda da hakan dakyar suka yarda suka fito Tsoron mutanen garin suke da tarin gine ginen dasuka gani ya daga musu hankali tayi saudat sunan matar uncle tayi alkawarin nuna musu yadda zasu dinga kula da jikinsu Dan gabansu har wari yake dukansu da wani yauki saboda rashin kula gashi ko kamar zaka kitsa kansuma abun kallone ga gashi Amma Duk kwarkwata inbame dauriya ba baze iya zaman minti biyar dasu ba

Tayi mamaki da suhail ya iya tahowa dasu duk da Taji labarinsu Amma tayaya suhail yazama Dan wannan garin zata so taji suka rankaya gidan su suhail sukai horn me gadi ya bude musu sukai parking sai rike hannayensu take haka suka shiga gidan hankali kwance ma aikatan gidan gudu suke gani suke suhail fatalwane suka shiga parlour din sukai sallama alhaji da hajiya na zaune inalillahi wainna ilaihirrji'un muryar wanake ji kamar ta suhail nine mom da sauri ta juyo

Da gudu ya karasa shigewa jikinta mom sai kuka dad ko mutuwar zaune yai Yana kallonsu ya sake ta ya rungume daddy hamdala kawai yake dad mom da Baki fa nake Uncle yai murmushi kugama murnar sa shigo saudat ku shigo Mana cikin murmushi ta sawo Kai yammatan suka biyo bayanta a firgice daa ya Mike Suma suka mike gaba dayansu kawai gani sukai ya yanke jiki ya Fadi yanata nuna wani guri hankalinsu ya gama tashi gaba dayansu tofa fans meke faruwane dad yayi hamo

_To fans bari indakata anan inajin dadin comment dinku fans Ina kaunarku har raina muna tare iya wuya I love you Lodi Lodi masoyana💋💋💋💋_

*FEEDYN BASH*
[10/23, 2:33 PM] 👯🏻Ummu Subai'a🎭: *🎭ARNAN DAJI🎭*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

